# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Manomi da iri



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: M. Maillot; Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: E. Frischbutter; Sarah S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**Wata rana Yesu yana koyarwa a bakin ruwa. Mutane da yawa suka taru domin su saurare shi.**

**Taron jama’a ya yi yawa. Mene ne Yesu zai yi?**



**Da ganin dan jirgin ruwa kusa a wurin, Yesu ya shiga ciki. Yanzu zai iya ganin mutanen kuma su za su iya ganin shi su kuma ji shi.**



**Yesu ya fara magana a cikin misalai – labarai game da abubuwa na yau da kullum, masu koya wa mutane game da Allah.**



**“Wani manomi ya baza iri a filinsa,” labarin Yesu kamar hoto ne mai kalmomi maimakon zane-zanen hotuna.**



Mutane suna iya ganin hoton wani manomi yana aiki – suna ganinsa sau da dama.



Wadansu irin suk bazu a hanyar da ake bi da kafa. Haya! Nan da nan sai tsuntsaye suka sauka kasa suka kwakwashe.



**Wadansu iri suka faffadi a gefen fili inda akwai duwatsu. Nan da nan suka yi girma amma babu karfi. Da zafin rana ya bullo sai rana ta cinye su suka bushe saboda tushinsu bai yi karfi ba.**





**Wadansu iri suka fadi a cikin kaya. Ba su haifar da 'ya'ya ba. Kayoyin 'ya'yan sun kewaye 'yan tsirorin, sun hana su samun rana da ruwan sama.**

**Sauran irin sun faffadi a kasa mai kyau. Yayinda lokaci yana wucewa, tsirorinsu suka zama lafiyayyu suka haifar da sabobbi hatsi masu yawa. Lallai kam, manomin zai kasance da farin ciki!**



**A karshen labarin, almajiran suka zo wurin Yesu. “Don me kake koyarwa a cikin misalai?” suka tambaya.**



**Yesu ya ce misalai sukan taimaki mutane su gane game da Allah idan suna kaunarsa da gaske. Mutanen da ba sa kaunar Allah ba za su gane misalai ba.**




Yesu ya bayana misalin. Ya ce irin shi
ne Kalmar Allah. Iri a hanyar da kafa ke
bi shi kamar jin magana ne amma babu
ganewar Kalmar
Allah. Ibilis yakan
sa sus u manta
abunda
Allah ya
fada.

Wadansu sukan karbi Kalmar Allah da sauri-sauri. Su kamar iri wanda ya fadi a kasa mai duwatsu ne. Amma muddin wani ya yi musu gori ko a tsananta musu saboda suna kaunar Allah, sai abu mumuna ya faru.



**Wadannan mutanen da suka fara bin Yesu cikin farin ciki za su juya baya su bar yin biyayya ga Kalmar Allah. Ba sa so su biya firashin bin Allah. Abin bakin ciki ne domin suna so su yi abin da abokan su ke so ne ba abin da Allah yake so ba.**



**Kayoyin a cikin misalin suna nan kamar damuwoyin duniya da son kudi wadanda sun cika rayuwar wadansu mutane. Suna cikin nemaan kudi da kayan duniya kamar babu gobe har sun bar Allah a waje daga rayuwarsu.**



**Amma irin da ya fadi a kasa mai kyau ya ba da amfanin gona yana kama da Kalmar Allah wadda take shiga zukata tana kuma canja rayuwar mutane. Mutanen nan suna hidima da daukaka ga Allah.**



**Taron jama’a ba su so bari ba. Yawancinsu sun so su bi Allah su kuma faranta masa rai. Labarai cikin misali na Yesu ya taimake su su gane yadda za a yi wa Allah biyayya.**



# Manomi da iri

# Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

# a na samu a

# Matiyu 13

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

43

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**